# Ƙirƙirarren Tunani

Mahalarta taron za su bincika yanda fitattun ‘yan wasu da labarai za su iya da kuma yanda aka yi amfani da su wajen inganta wayar da kai jama’a da kuma fafutuka a ɗaukacin sanadin. Mahalarta taron za su gano fitaccen ɗan wasa guda ɗaya da kuma labarin da za a iya amfani da shi wajen inganta wayar da kan jama’a dangane da wani sanadi da ke da muhimmanci a gare su.

# Fitacce Ɗan Wasa da Fafutuka

## Kashi na Ɗaya

**Sanar da Ɗalibanka**

Zana hotuna, darussa, ko misalai daga ‘yan wasa a ciki litattafan da ka fi so, fina-fanai, da wasannin TVn za su iya kasancewa hanyar da ta fi dacewa wajen wayar da kawunan jama’a dangane da sanadin. Sau da yawa, ƙwarewar da ake da ita a kan ƙirƙirarrun ‘yan wasa za ta iya rinjayar tunanin mutane game da matsalolin zahiri a duniya.

Misali, halin da Harry Potter ya nuna dangane da house-elves zai iya jawo damuwa da yawa game bautar da yara ko yanayin aiki mara kyau a wajen ƙirƙirar abubuwa. Bayan fitowar Avatar na James Cameron, an samu ƙaruwar masu sha’awa a fafutukar kare muhalli. ‘Yan wasan da ake sha’awa suna da tasiri wajen shafar canje-canjen halayyar mutane da yawa, da kuma inganta su don yin amfani da su a waje fafutukar wayar da kawaunan jama’a.

A kan allon majigin, nuna wani bidiyo na kwanan nan da aka shirya tare da / mahalarta taronka na cikin gida / wani rubutu a yankin don ci gaba da ƙarfafa manufar ta hanyar yin amfani da fitacciya al’ada wajen wayar da kan jama’a dangane da sanadin. Wani misali daga wani rubutu a Kasar Amurka (a Ingilishi) shi ne Masoyan Harry Potter da Ya Yi Nasara a Kan Bautar da Kananan Yara daga Harry Potter Alliance. Bayan an nuna bidiyon, yi bayani a kan dalilin da ya sa ka zaɓi wannan bidiyon da kuma dalilin da yasa ka yarda cewa misali ne mai kyau wajen inganta wayar da kan jama’a dangane da matsalar ta hanyar fitacciyar al’ada.

**Sanar da Ɗalibanka**

A cikin wannan aikin da ke tafe, za ka samar da taka fafutukar wayar da kawunan mutanen ta hanyar yin amfani da fitaccen ɗan wasa ko labari.

# Aiki

## Kashi na Ɗaya

### Sanar da Ɗalibanka

Za mu zagaye ɗakin sannan mu nemi kowane mutum da ya faɗi sunayen wasu ‘yan wasa ko labarun da ya fi so.

### Tattaunawa a Aji

Ka nemi mahalarta taron da su faɗi sunayen ‘yan wasa guda biyu ko guda uka ko kuma labaran da suka fi so. Bayan haka, shirya ɗalibai zuwa rukunoni guda 3 bisa ga makamantan abubuwan da suke sha’awa.

### Sanar da Ɗalibanka

A matsayin ƙungiya, gano ɗan wasa ko labarin da za ka iya yin amfani da shi wajen yin magana a kan matsalar da ke da muhimmanci a gare ka.

A matsayin ƙungiya, rubuta amsoshin waɗannan tambayoyin:

1. Wane ne fitattcen ɗan wasanka ko labari?

2. Wace matsala ce kake so ka yi magana a kanta ta hanyar yin amfani da ɗan wasan ko labarin

3. Wane fim, kiɗa, ko ƙagaggun labaran duniya ne za ka gina fafutukarka a kai?

4. Yaya za ka samar da kafar watsa labarai (misali., waƙa, zane mai ban dariya, kwalin sanarwa, da dai sauransu) a kan fom ɗinka na fitaccen ɗan wasan da ka fi so don wayar da kan jama’a dangane da matsalar da ka zaɓa?

5. Yaya za ka raba wannan aikin a kan intanet da kuma cimma masu sauraro da yawa?

Wannan kayan karantarwar da Matasa da Kafar Watsa Labarai suka samar a Cibiyar Samar da Intanet &amp ta Berkman Klein; Jama'a a Jami'ar Harvard a ƙarƙashin lasisin Creative Commons Attribution-ShareAlike 4.0 International. Za ka iya yin amfani da wannan, har da yin kwafi da kuma shirya samar da ayyuka, ko kuɗi ko kuma wanda ba na kuɗi ba, kamar yanda ka siffanta. Matasa da Kafar Watsa Labarai a matsayin tushen da suka samar da ayyukan na ainihi da kuma raba wasu ayyukan da za su zo a gaba a ƙarƙashin sharuɗɗa ɗaya. Waɗannan da wasu ƙarin kayayyakin karantarwar su ma akwai su a intanet a Dandalin Kayayyakin Karatu da Rubutun Zamani na Berkman Klein.